# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Kaunatacce Da ya zama Bawa



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Byron Unger; Lazarus**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: M. Kerr; Sarah S.**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan har ba zaku sayar da shi.**



**Ishaku ya kasance cike da farin ciki.  Dansa Yakub ya dawo gida.  Har ma Isuwa ya marabce dan'uwansa wanda ya rantse cewa zai kashe shi.  Amma 'ya'ya maza na Yakub ba su ji dadi ba saboda Yusuf, kaninsu, wanda shi ne babansu ya fi so.**



‘Yan’uwan Yusuf sun karu da haushi sa’ad da ya gaya musu mafarkinsa. “Daurin hatsina ya fi na ‘ya’uwana tsayi,” Yusuf ya ce. Wannan mafarki ya nuna cewa Yusuf zai fi sauran ‘ya’uwansa muhimminci.



3

A mafarki na biyu na Yusuf, rana, da wata, da taurari suna sunkuya suna bauta masa. Har ma da mahaifinsa Yakub ya ji fushi da shi domin ya sa kansa a bisan iyayensa da ‘yan’uwansa.



4

Wata rana Yakub ya aike Yusuf zuwa filin kiwo inda ‘yan’uwansa suke kiwon tumakansu. ‘Yan’uwansa suka hange shi daga nesa yana zuwa. “Bari mu kashe wannan mai mafarki,” suka ce wa juna. Yusuf kuma bai san barazanan da ke gabansa ba.



5

Ruben, da na fari bai yarda ba. “Ba za mu zub da jini ba,” ya ce. “Dubi, ga wani rami. Bari ya mutu a wurin!” Ruben yana shiri ya kubutar da shi da daddare.



6

Lokacin da Yusuf ya kai, sai ‘yan’uwansa suka cafke shi, suka cire tufafinsa masu kala-kala wadanda mahaifinsu Yakub ya dinka masa na musamman na dansa wanda ya fi so. Sai suka jefar da shi a mummunan ramin.



7

Sa’ad da Ruben ba ya nan, sai kungiya na masu rakumai suna tafiya zuwa kasar Masar. “Bari mu sayar da Yusuf,” Yahuda dan’uwansa yayi ihu.
Sai a ka yi ciniki.





Suka sayar da Yusuf a kan azurfa ashirin.

8

Cike da hawaye da tsoro, Yusuf yana kallo yadda ana tafiya da shi a kan rakumai ana raba shi da iyalinsa da kasarsa.



9

“Wannan ba shi ne rigar Yusuf ba? Ga shi jike da jini. Mun same shi a hamada.” Waddanan mugayen ‘yan’uwa sun sa Yakub ya yarda cewa mugayen dabbobin daji ne sun cinye kaunataccen dansa. Yakub ya yayyage rigunansa ya yi makoki. Babu wani wanda ya iya ta’azantar da shi.



10

A Masar, Yusuf ya kasance cikin tsoro da zaman kadaici. Watakila ya yi marmarin komawa gida. Amma babu yadda zai kubce. Shi bawa ne a gidan Fotifa wani babban mutum a Masar. Fotifa ya gan cewa Yusuf yana da kwazon aiki kuma za a iya amince da shi.



11

“Kowane abu wanda ka yi yana yin kyau,” Fotifa ya gaya wa Yusuf wata rana. “Allah yana tare da kai. Ina so ka zama shugaba na masu yi mini hidima, kana lura da harkan kasuwancina ka kuma zama maigidan duka masu yi mini hidima.”



12

Allah ya ba wa Fotifa girbi mai yawa da arziki da dama saboda Yusuf. Ko da yake yanzu ya zama mutum mai martaba, duk da haka ya yi wa Ubangiji hidima cikin aminci da gaskiya. Amma damuwa ta taso wa Yusuf.



13

Matan Fotifa muguwar mace ce. Ta gaya wa Yusuf ya dauki matsayin maigidanta. Yusuf ya ki. Ba zai yi zunubi ga Allah ta wurin cin amana Fofifa ba. Sa’ad da macen ta yi kokari ta tilasta shi, sai ya gudu. Amma ta kama ta rike rigarsa.



14

"Bawanka ya kawo mini hari," in ji matan Fotifa tana gunaguni. "Dubi, ga rigarsa!" Fotifa ya yi fushi. Watakila ya sani cewa karya ne matansa take yi. Amma dole ne ya yi wani abu. Mene ne zai yi?



15

Fotifa ya sa Yusuf a kurkuku. Ko da yake ba shi da laifi, Yusuf kuwa bai bata rai ko ya yi fushi ba. Watakila yana koyo ne daga wahalolinsa cewa ko da a ina ne yake, in ya girmama Allah, Allah zai daukaka shi – ko da ma a kurkuku ne.



16

Kaunatacce Da ya zama Bawa

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Farawa 37, Farawa 39

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

17




7 60

18

Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.

Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.

Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:
Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.

Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16

19